# DOKAR 'YANCIN SAMUN BAYANAI TA 2011

RIGHT TO KNOW

Da taimakon

OPEN SOCIETY INITIATIVE FOR WEST AFRICA

# DOKAR ’YANCIN SAMUN BAYANAI TA 2011

## GABATARWA

Wannan doka za ta bayar da damar samun adanannun takardu da bayanai a wadace ga jama’a ba tare da matsala ba, kuma ta kare adanannun takardu da bayanai ta yadda za su dace da bukatun al’umma da kare sirrin daidaikun mutane da kare ma’aikaci daga musgunawa saboda ya bayyana wadansu bayanai da suka shafi hukuma ba tare da izini ba, kuma ta tsara hanyoyin da za a bi don cimma wadannan manufofi.

# DOKAR ’YANCIN SAMUN BAYANAI TA 2011

## TSARIN SASSA

### Sashi

1. Yancin samun adanannun takardu da bayanai.
2. Bayanai game da hukumomin gwamnati.
3. Neman izinin ganin adanannun takardu.
4. Lokacin amincewa ko kin amincewa da bukatar.
5. Tura takardar bukatar zuwa wani wuri na daban.
6. Kara tsawon lokacin da aka kayyade na amincewa ko kin amincewa da takardar bukata.
7. Idan aka ki bada izini.
8. Biyan kudade.
9. Adana takardun bayanai da kula da su.
10. Lalatawa ko jirkita bayanan.
11. Tsame al’amuran da suka shafi harkokin kasashen waje da tsaro.
12. Tsame hukumomin tabbatar da bin doka da gudanar da bincike.
13. Horar da jami’ai kan ’yancin samun bayanai da yadda za a aiwatar da wannan doka yadda ya kamata.
14. Tsame bayanan da suka shafi sirrin wani.
15. Tsame bayanan da suka shafi sirrin mutum na uku.
16. Tsame bayanin da ya shafi sirrin wani ko wasu alfarmomi da doka ta amince da su.
17. Tsame takardun kwasa-kwasai ko bincike.
18. Yawa
19. Kiyawar wata hukumar gwamnati ta bayar da adanannun bayanai.
20. Sake duba dokar.
21. Sauraren kara ta takaitacciyar hanya.
22. Samun bayanai ta kotu.

23. Umarnin kotu kan hana bayar da bayanai.
24. Alhakin gabatar da hujja.
25. Umarnin bayar da bayanai.
26. Takardun bayanan da aka tsame.
27. Kariya ga jami'an gwamnati.
28. Wadansu muhimman takardu.
29. Mika rahotanni.
30. Matakai masu karfafawa.
31. Fassara.
32. Bita.

# DOKAR ’YANCIN SAMUN BAYANAI TA 2011

Kudiri

Don

Kafa dokar da za ta sa adanannun takardu da bayanai su zamo a wadace kuma a ba jama’a damar iya samunsu babu matsala, kuma ta kare adanannun takardu da bayanan ayyukan gwamnati ta yadda za su dace da bukatun al’umma da kare sirrin rayuwar daidaikun mutane, kuma ta kare ma’aikaci daga musgunawar da za ta auku gare shi saboda bayar da bayanan da suka shafi hukuma ba tare da izini ba, kuma ta tsara hanyoyin da za a bi don cimma wadannan manufofi da abubuwan da suka danganci haka.

Majalisar Dokoki ta Tarayyar Nijeriya ta tabbatar da ita a matsayin doka-

1. (1) Ba tare da lura da duk wani abu da ke kunshe a kowace doka ko kudirin doka da ka’ida ba, ’yancin kowane mutum ya samu ko ya nemi a ba shi bayanai ya-alla suna adane a rubuce ne ko a’a, da suke a karkashin kular wani ma’aikacin gwamnati ko hukuma ko cibiya da aka bayyana ko aka tabbatar.

(2) Duk wanda ke neman bayani a rubuce a karkashin wannan doka ba lallai ne ya bayyana dalilinsa na sha’awar neman wannan bayani da yake yi ba.

(3) Kowane mutum da ke da ’yancin samun bayanai a karkashin wannan doka, wajibi ne ya shigar da kara a kotu don sanya duk wata hukumar gwamnati ta yi aiki da wannan doka.

2. (1) Kowace hukumar gwamnati wajibi ne ta tabbatar ta adana takardun bayanan ayyukanta da abubuwan da ta gudanar ko kayayyakin da aka yi cinikinsu.

(2) Kowace hukumar gwamnati ta tabbatar ta tsara tare da kula da dukkan bayanan da suke hannunta yadda ya kamata ta yadda za ta bayar da dama ga jama'a su samu wadannan bayanai.

(3) Kowace hukumar gwamnati wajibi ne ta buga bayanai masu zuwa kamar yadda karamin sashi na (4) na wannan sashi ya nema-

(a) fasalin yadda tsarin ayyuka da nauyin da ke kan hukumar ciki har da dalla-dallar tsare-tsare da aikin kowane bangare ko reshe ko sashin hukumar;

(b) jerin dukkan-

(i) ajujuwan adanannun bayanai da ke karkashin hukumar ta hanyar wadatattun bayanai dalla-dalla don ba da 'yanci ga masu neman bayani a karkashin wannan doka,kuma

(ii) Takardun da ma'aikata suka rubuta da hannu wajen gudanarwa ko aiwatar da kowane shiri ko ayyukan hukumar;

(c) Bayyana takardun da suke dauke da shawarwari na karshe ciki har da inda ra'ayi ya zo daya ko aka samu sabani da kuma umarnin da aka bayar wajen yanke shawara kan al'amuran;

(d) takardun da suka kunshi-

(i) muhimman ka'idojin hukumar,

(ii) bayanai da ma'anonin tsare-tsare da hukumar take amfani da su,

(iii) tsare-tsare ayyuka na karshe da shawarwari da hukuncin da aka yanke;

(iv) rahotannin ayyuka da na ziyarar duba ayyuka da nazarce-nazarce da hukumar ta shirya ko aka shirya mata;

(v) bayanan da suka shafi karba da kashe kudaden gwamnati ko sauran kudaden hukumar;

(vi) sunaye da albashi da mukamai da ranakun da aka dauki dukkan ma'aikata da jami'an hukumar;

(vii) sunan duk wani jami'i da shawarar karshe da aka yanke a dukkan ayyukan hukumar;

(e) jerin-

(i) fayi-fayil da ke kunshe da takardun neman duk wata kwangila ko takardar biyan kudi ko ta samun kudi ko ta lasisi ko yarjejeniyoyi,

(ii) rahotanni da takardun bayanai da nazarce-nazarce ko takardun da 'yan kwangila masu zaman kansu suka tsara wa hukumar da

(iii) kayayyakin da suke dauke da bayanan da suke da alaka da duk wani kudin da hukumar ta samu ko yarjejeniyar da hukumar ta kulla tsakaninta da wata hukumar gwamnati ko wata cibiya mai zaman kanta;

(f) matsayi da adireshin duk wani jami'in da ya cancanci a rubuta masa wasikar neman bayanai a karkashin wannan doka, kuma da wata hukumar gwamnati za ta gaza buga

wani bayani a karkashin wannan karamin sashi hakan ba zai hana jama'a damar samun bayanan da suke karkashin kulawar wannan hukuma ba.

(4) Kowace hukuma ta gwamnati wajibi ne ta tabbatar bayanan da ake batu a kansu a wannan sashi ya zamo an watsa su kuma sun kasance a shirye cikin wadata ga jama'a ta hanyoyi da dama ciki har da kafafen labarai kamar jaridu da gidajen rediyo da talabijin da intanet da kuma ofisoshin hukumar.

(5) Kowace hukumar gwamnati wajibi ne ta rika tsarawa da sake duba bayanan da ake bukata don bugawa a karkashin wannan sashi a lokuci-lokuci da kuma da zarar an samu canje-canje.

(6) Duk mutumin da ya cancanci samun bayanan da wannan doka ta amince yana da ikon shigar da kara a kotu don tilasta kowace hukumar gwamnati ta yi aiki da tanade-tanaden wannan sashi.

(7) Hukumomin gwamnati sun hada da duk hukumomi, ya-alla cibiyoyi da hukumomin bangaren zartarwa ne ko na majalisa ko na shari'a da ma'aikatu da rassan ma'aikatu da sassan ma'aikatun gwamnati tare da dukkan kamfanoni da hukumomin da doka ta kafa su da kuma dukkan kamfanonin da gwamnati ke da jari mafi girma a cikinsu da kamfanoni masu zaman kansu da suke amfani da kudaden gwamnati ta wajen yi wa jama'a aiki ko aiwatar musu da wadansu hidimomi.

3. (1) Takardar bukatar adanannun takardu ko bayanai a karkashin wannan doka wajibi ne su kasance kamar yadda sashi na 1 na wannan doka ya tanada,

(2) Don cimma manufar wannan doka, duk wani bayani ko takardun bayanai da aka nema a karkashin wannan doka da ba

a buga su ba, amma za iya fito da su daga wata na'ura da a galibi gwamnati ko hukumomin gwamnati ke amfani da ita, za a dauke su a matsayin adanannun bayanai da suke karkashin kular gwamnati ko hukumar gwamnati.

(3) Marar ilimi ko nakasasshen da suke bukatar bayanan amma saboda jahilci ko nakasar da suke fama da su ba za su iya rubuta takardar neman bayanan ko adanannun takardun ba kamar yadda tanadin karamin sashi na (1) na wannan sashi ya nema, suna iya rubuta takardar bukatar ta hannun wani mutum.

(4) Idan mai neman takardun bayanai ya tuntubi jami'in gwamnati ko na wata hukumar gwamnati da aka ba izinin a tuntuba da fatar baka, jami'in yana iya mayar da bukatar ta zama a rubuce daidai yadda karamin sashi na (1) na wannan sashi ya nema kuma ya mika kwafen rubutacciyar bukatar ga mai neman.

4. Idan aka rubuta takardar neman bayanai a karkashin wannan doka, hukumar gwamnati da aka rubuta wa bukatar bisa tanadin sashi na 6 da na 7 da na 8 na wannan doka cikin kwanaki bakwai da karbar rubutacciyar bukatar za ta-

(a) Mika bayanan ga wanda ya nema;

(b) Idan wata hukumar gwamnati ta ga akwai bukatar ta ki amincewa da bukatar, to za ta bayar da bayani a rubuce ga mai bukatar cewa ba za a iya ba shi wani bangare na bayanan ko dukkansa ba, inda za ta bayyana dalilan hanin da kuma sashin da ta dogara da shi don yin haka a karkashin wannan doka.

5. (1) Idan wata hukumar gwamnati ta karbi takardar bukatar neman bayanai, kuma ta ga cewa wata hukumar gwamnati ta daban na da babbar sha'awa kan bayanan, cikin kwanaki uku zuwa bakwai bayan karbar takardar bukatar za ta mika takardar bukatar idan zai yiwu har da bayanan ga waccan hukuma,

kuma idan hakan ta samu hukumar za ta rubuta takardar sanar da mai bukatar game da tura bukatar ga waccan hukuma takardar da a ciki za ta kunshi bayanan sanar da shi cewa wancan shawara ta tura bukatar ana iya kalubalantarta a kotu.

(2) Idan aka sauya wa takardar bukata zuwa wani wuri bisa dogaro da karamin sashi na (1), takardar bukatar za a mika ta ga hukumar gwamnatin da aka mayar da bayanan gare ta a ranar da hukumar ta karbe su.

(3) Don cimma bukatar karamin sashi na (1), hukumar gwamnati tana da "babbar sha'awa" ga bayanai idan-

(a) tun asali ita ta fitar da bayanan ko an fitar da dominta; ko

(b) idan tun asali bayanan ba daga wurinta suka suke ba, ko ba dominta aka fitar da su ba, amma hukumar ce hukumar gwamnati ta farko da ta fara samun bayanan.

6. Hukumar gwamnati tana iya kara tsawon lokacin da aka tsara a sashi na 5 ko na 6 dangane da wata rubutacciyar bukata zuwa wani lokaci da ba zai haura kwanaki bakwai ba idan-

(a) takardar bukatar tana neman adanannun bayanai da takardun tarurruka masu dimbin yawa, to lokacin da aka kayyade na farko yana iya kawo cikas ga gudanar da ayyukan hukumar; ko

(b) Tuntuba tana da muhimmanci domin ganin an biya bukatar takardar neman bayanan wadda ba lallai ba ne a cimma nasarar hakan a cikin lokacin da aka kayyade, ta hanyar bayar da sanarwar kara lokaci tana mai bayyana ko karin lokacin ya fado karkashin dalilan da ke karkashin wannan sashi, inda sanarwar za ta kunshi bayanin cewa marubucin bukatar yana da 'yancin ya kalubalanci karin wa'adin a kotu.

7. (1) Idan gwamnati ko wata hukumar gwamnati ta ki bayar da adanannun takardu ko bayanan da aka nema a karkashin wannan doka ko wani bangare na bayanan to wannan hukuma za ta sanar da wanda ya nemi a ba shi bayanan dalilan kin ba shi tare da kawo hujjar haka karkashin tanadin wannan doka a sanarwar da za ta ba shi, kuma ta bayyana masa cewa yana da 'yancin da zai kalubalnaci wannan shawara kuma yana iya samun nasara a warware wannan shawara a kotu.

(2) Takardar sanar da kin karbar rubutacciyar bukatar neman bayanan ko adanannun takardu wajibi ne ta bayyana suna da mukami da sa hannun duk mutumin da alhakin hanawar ke kansa.

(3) Gwamnati ko hukumar gwamnatin za a bukaci su bayyana ko wannan bayani ko adanannun takardu akwai su, kamar yadda ke kunshe a karamin sashi na (1) na wannan sashi.

(4) Idan gwamnati ko hukumar gwamnati ta gaza bayar da bayanai ko adanannun takardun da aka nema a rubuce a karkashin wannan doka ko wani bangare nasu, a lokacin da aka kayyade, kamar yadda ke kunshe a wannan doka, to a karkashin wannan doka za a dauka hukumar ta ki bayar da bayanan ne.

(5) Idan aka tabbatar an hana bayanan bisa kuskure, jami'in da ya yi laifin ko hukumar sun aikata laifi, kuma idan kotu ta tabbatar da laifi a kansu za a iya cin tararsu Naira dubu 500.

8. Kudaden da za a biya don buga takardun bayanan ko juya su daga kaset zuwa rubutu idan ta kama za su kasance madaidaita ne.

9. (1) Kowace gwwamnati ko hukumarta wajibi ne su tabbatar sun adana dukkan bayanai ko takardun da suka shafi harkokin hukumar da na ma'aikata da ayyuka da makamantansu ko sauran bayanai da takardun da suka shafe su.

(2) Kowace gwamnati ko hukumar gwamnati wajibi ne ta tabbatar tana tsarawa da kula da dukkan bayanai ko adanannun takardun da ke karkashin kularsu ta hanyar da za su bayar da dama ga jama'a su samu wannan bayanai da takardu a karkashin wannan doka.

10. Babban laifi ne da za a yi hukunci a kai idan kotu ta tabbatar da shi,inda za a yanke hukuncin daurin shekara daya a kurkuku ga duk wani jami'i ko shugaban wata gwamnati ko hukumar gwamnati wadda wannan doka ta shafa amma aka samu sun lalata kowane adanannen bayani da aka ajiye a karkashin kularsu ko suka yi kokarin jirkita shi ko cire wani abu kafin su ba duk wani mutum ko wata cibiya ko al'umma da suka bukaci a ba su.

11. (1) Kowace hukumar gwamnati tana iya kin amincewa da takardar bukatar samun kowane bayani da bayyana shi zai iya illa ga tsarin harkokin kasashen waje ko tsaron Jamhuriyar Nijeriya.

(2) Ba tare da warware karamin sashi na (1) ba, za a hana takardar bukatar neman bayanai a lokacin da alfanun bayar da bayanin zai fi amfanar jama'a fiye da illar da bayyanawar za ta jawo.

12. (1) Hukumar gwamnati tana iya kin amincewa da bukatar bayar da kowane bayani da ya kunshi-

(a) Adanannun bayanai na wata hukumar gwamnati don gudanar da bincike ko wadanda wata hukumar tsaro ko ta tabbatar da bin doka da oda ko hukumar gyaran xabi'u don tabbatar da bin doka da oda ko harkokin cikin gidan wata hukumar gwamnati, idan ya zamo bayyanawar za ta-

(i) kawo cikas ga binciken ko za ta yi matukar kawo cikas ga ayyukan da wata hukumar tabbatar da bin doka da oda ko cibiyar gyara halaye za ta yi,

(ii) kawo cikas ga aiwatar da wata shari'a ko zaman bincike da wata hukumar gwamnati ta gudanar,

(iii) zai hana a saurari wani mutum bisa adalci, ko ya hana shi samun adalci yayin gudanar da shari'a.

(iv) ko duk yadda aka yi za a bayyana hakikanin wata majiya mai tushe da bai kamata ba,

(v) ko zai jawo a shiga cikin harkar rayuwar mutum ta kashin kai da sashi na 15 na wannan doka ya ba shi dama, matukar ba bukatar jama'a ce ta fi dacewa ta hanyar samun wannan bayani ba, wannan tsarewa na bayyanawa ba za a yi aiki da shi ba,

(vi) zai hana gudanar da bincike kan babban laifi; ko

(b) bayar da bayanin da ake ganin zai iya kawo illa ga harkar tsaron hukumomin bincike.

(2) Ba tare da warware wani abu da ke kunshe a wannan sashi ba, ba za a ki karbar bukatar bayar da bayani ba, idan bukatar jama'a ta samun bayanin ta fi duk wata illa da bayyanawar za ta jawo.

(3) Hukumar gwamnati tana iya kin amincewa da takardar bukatar neman bayanin da ake jin zai iya bayar da damar aikata wani laifi.

(4) Bisa ga manufar sashi na (1) (a), kalmar "don gudanar da bincike" tana nufin binciken da-

(a) ya shafi aiwatarwa ko tilasta aiki da kowace doka ko ka'ida;

(b) aka bayar da izini ko don cika umarnin wata doka ko ka'ida.

13. Kowace gwamnati ko hukumar gwamnati wajibi ne ta tabbatar tanadin da ya dace na horar da ma'aikatanta kan 'yancin jama'a ga samun bayanai ko adanannun takardun da suke hannun gwamnati ko

hukumomin gwamnati, kamar yadda wannan doka ta tanada domin samun nasarar aiki da wannan doka.

14 (1) Bisa dogaro da karamin sashi na (2) wajibi ne hukumar gwamnati ta ki karbar bukatar bayar da bayanan da suka kunshi bayanin sirrin rayuwar ma'aikaci ko bayanin da aka tsame a karkashin wannan sashi da ya hada da-

(a) Fayil-fayil da bayanan suka shafi sirrin abokan harka ko marasa lafiya ko mazauna wuri ko dalibai ko sauran daidaikun mutane da suke karbar tallafin inganta rayuwa ko na magani ko na ilimi ko na koyon sana'a ko na kudi ko sanya ido ko raino ko yin aiki kai-tsaye ko a kaikaice daga hukumomin gwamnati;

(b) Fayil-fayil din ma'aikata da bayanan da suka shafi rayuwar sirri ta ma'aikata ko wadanda aka nada ko zababbun jami'ai ko duk wata hukuma ko mai neman wadancan mukamai;

(c) Fayil-fayil da bayanan da suka shafi rayuwar sirri ta mai neman aiki ko mai rajista ko mai neman lasisi daga kowace gwamnati ko hukumar gwamnati da take gudanarwa ko aka ba alhakin aiwatar da aiki ko rajistar ayyukan ko bayar da lasisi ko bayar da horo;

(d) Bayanan da aka nema na wani mai biyan haraji don auna ko karbar kowane haraji matukar ba wata doka ce ta nemi a bayyanar ba; ko

(e) Bayanin da zai fallasa mutanen da suka aika da qorafi ko kuka ko suka bayar da bayani ga masu gudanar da bincike ko jami'an tsaro ko hukumomin bincike kan hukumar ko kowane laifi.

(2) Hukumar gwamnati tana iya bayar da kowane bayani da ya kunshi bayanan sirrin rayuwar mutum idan-

(a) wancan mutum yana da alaka da bayanin da ake son bayyanawa; ko

(b) bayanan sun watsu a tsakanin jama'a.

(3) A duk inda aka ambaci bayar da bayanai a karkashin wannan sashi wajibi ne ya zama don bukata da amfanin jama'a ne, kuma idan sha'awar jama'a ga bayar da bayanin ta fi batun kare sirrin wani mutum da bayanin ya shafa, hukumar gwamnati da aka nemi ta bayar da bayanin wajibi ne ta bayar da shi kamar yadda yake kunshe a sashi na 14 (2) na wannan doka.

15. (1) Hukumar gwamnati tana iya kin amincewa da bukatar bayar da bayanin da ya kunshi-

(a) cinikayyar sirri ko kasuwanci da bayanan harkokin kudi da aka samu daga wani mutum ko cibiyar kasuwanci da irin wadannan cinikayya na sirri ne, ko bayanai masu muhimmanci ko amana da ba tilas ne a bayyana su ba, ko bayyana cinikayyar sirrin ko bayanan suna iya cutar da bukatar mutum na uku, matukar ba wani abu a wannan karamin sashi da za a kirkira don a hana wani mutum ko cibiyar kasuwanci daga neman a yi bayanin.

(b) bayanin da idan bayar da shi ana kyautata zaton zai kawo kafar ungulu ga yarjejeniya ko wasu tattaunawa da mutum na uku; ko

(c) mika bukata da neman wata kwangila ko tallafi ko yarjejeniya ciki har da bayanin da in aka bayar zai hana a saya ko a taimaki wani mutum.

(2) Hukumar gwamnati ba tare da warware karamin sashi na (1) ba, tana iya bayar da bayanin wani bangare na takardun da

suka kunshi sakamako ko gwajin muhalli da wata hukumar gwamnati ta gudanar ko aka gudanar a madadinta.

(3) Idan hukumar gwamnati ta bayar da bayani ko wani bangare na bayani da ya kunshi gwajin wani kaya ko na muhalli, a lokaci guda tana iya bayar da bayanin ko wani bangarensa, ga mai bukatar bayanin a rubuce kan hanyar da aka bi aka gudanar da gwajin.

(4) Hukumar gwamnati tana iya bayar da kowane bayani da aka ambata a karamin sashi na (1) na wannan sashi idan bayar da bayanin zai kasance don amfanin jama'a kan abin da ya shafi lafiyar jama'a da kare rayukan jama'a ko kare muhalli, kuma idan sha'awar bayar da bayanin daga jama'a ta fi zama mai muhimmanci balo-balo kan asarar kudi ko wata riba, kuma ba za ta kawo nakasu ko tsoma baki ga kwangila ko yarjejeniyar da aka kulla da mutum na uku ba.

16. Hukumar gwamnati tana iya kin amincewa da bukatar samun bayani da ya shafi damarmaki masu zuwa-

(a) lauya – sirrin wanda yake karewa

(b) ma'aikacin lafiya – sirrin mai jinya

(c) aikin jarida – damar boye majiyar labari; da

(d) sauran sirri na kwararru da doka ta bayar.

17. Hukumar gwamnati tana iya kin amincewa da bukatar samun bayanin da ya kunshi takardun kwas ko bincike da jami'an sassan ilimi suka tsara.

18. Ba tare da lura da wani tanadi na wannan doka ba, idan aka mika bukatar samun bayanan da aka tsame su daga bayyanawa ga wata hukuma ta gwamnati bisa tanadin wannan doka, hukumar tana iya

bayyana wani bangare na bayanin da ba ya kunshe a cikin bayanan da aka tsame.

19. (1) Hukumar gwamnati tana iya kin amincewa da takardar bukatar neman bayanin da ya kunshi bayanan da suka shafi-

(a) tambayoyin gwaji ko makin da aka samu, da sauran bayanan jarrabawa da aka tsara don gudanar da jarrabawar ilimi ko a bayar da damar neman lasisi ko aiki.

(b) tsare-tsaren masu zayyana ko injiniyoyi don yin ginin da ba a kammala shi duka ba, ko wani bangarensa da ake yi da kudin hukuma ko ginin da aka gina da kudin hukuma ta yadda bayyanawar za ta iya haifar da matsala ga tsaro; da

(c) takardun dakunan karatu da sauran takardun da suke kunshe da bayanai masu amfani da wasu takardun da aka ambata a dakunan karatun:

(2) Ba tare da lura da wani abu da ke kunshe a wannan sashi ba, ba za a ki amincewa da takardar bukatar neman bayani ba, a lokacin da bukatar jama'a na neman bayanin ta fi duk wata illa da bayyanawar za ta haifar.

20. Duk wani mai bukata da aka hana shi samun bayani ko wani bangare nasa, yana iya neman kotu ta sake duba batun a cikin kwanaki 30 bayan hukumar gwamnati ta hana, ko ya dauka cewa ta hana bukatar, ko a cikin wani lokaci da kotun za ta ajiye ko ta yarda a gabani ko bayan karewar wa'adin kwanaki 30.

21. A hanzartar sauraron qarar da aka kai kotu kan bukatar da aka gabatar a karkashin sashi na 20.

22. Ba tare da lura da wani abu sabanin abin da ke kunshe a dokar Bayar da Shaida ko duk wata ka'ida a karkashinta ba, kotun a lokacin sauraron shari'ar da ke gabanta da ya taso kan wata takardar bukata

a karkashin sashi na 20 na wannan doka, za ta iya duba kowane bayani da wannan doka ta shafa wanda ke karkashin kulawar wata hukuma ta gwamnati, kuma ba za a boye wa kotun wannan bayani ba bisa kowane dalili.

23. A kowace shari'a da ke gaban kotu da ta samo asali daga wata bukata a karkashin sashi na 20 na wannan doka, kotun tana iya daukar matakin taka-tsantsan ciki har da lokacin da take karbar bayanan gabatarwa da sauraron shari'a a boye don kotun ta kauce wa bayar da bayani, ko bayyana wani mutum ko wani bayani ko sauran kayayyaki bisa dalilin da za a umarci wata hukumar gwamnati ta bayar da bayanin da aka nema.

24. A yayin sauraron kowace shari'a da ke gaban kotu kan abin da ya shafi bukatar neman bayani a karkashin sashi na 20 alhakin gabatar da shaidar cewa an umarci wata hukumar gwamnati ta ki amincewa da bukatar neman bayani ko bangarensa zai kasance ne a wuyan hukumar.

25. (1) A lokacin da hukumar gwamnati ta ki amincewa da takardar bukatar neman bayani ko wani bangarensa bisa wani tanadin wannan doka, kotu tana iya bayar da umarni ga hukumar ta bayar da bayanin ko wani bangarensa ga mai bukatar-

(a) idan kotun ta gano cewa ba a umarci hukumar ta ki amincewa da bukatar neman bayanin ba;

(b) idan an umarci hukumar kada ta bayar, amma kotun ta yanke shawarar cewa hukumar ba ta da kwakkwarar hujja ta kin amincewa da bukatar; ko

(c) idan kotun ta gano cewa bukatar jama'a ta samun bayanan ta fi muhimmanci daga alfanun da za a samu idan aka hana bayanan ta kowace fuska.

(2) Duk wani umarni da kotun ta bayar a karkashin wannan sashi zai kasance ne a karkashin ka'idojin da kotun take ganin sun dace.

26. Wannan Doka ba za ta yi aiki a kan-

(a) bugaggun takardu ko takardun da aka samar don sayarwa ga jama'a ba;

(b) takardun da suke dakunan karatu da na adana kayan tarihi ko aka saya aka adana domin jama'a su rika bincike a kai, ko don baje kolinsu ba; ko

(c) takardun da aka ajiye a Dakin Karatu na Qasa ko Gidan Adana Kayan Tarihi na Qasa, ko sashin da ba na hukuma ba a Dakin Adana Bayanai na Tarayyar Nijeriya a madadin wani mutum ko wata qungiya da ba gwamnati ba, ko wata hukumar gwamnati.

27. (1) Ba tare da lura da wani abu da ke kunshe a Dokar Manyan Laifuffuka da ta Kananan Laifuffuka da Dokar Boye Sirrin Hukuma ba, ba za a gabatar da wani ma'aikaci na kowace hukumar gwamnati ko duk wani mutum da ya yi aiki a madadin wata hukuma ta gwamnati kan karami ko babban laifi a kotu ba, kuma ba za a hukunta wannan mutum kan bayar da kowane bayani ko bangarensa bisa kyakkyawar niyya don bin wannan doka ba, babu wani mataki da za a dauka kansa saboda bayar da wannan bayani ko saboda gaza bayar da sanarwa kamar yadda aka nema a karkashin wannan doka idan an dauki matakin lura wajen bayar da sanarwar da aka bukata.

(2) Babu wani abu da ke cikin Dokar Manyan Laifuffuka da Dokar Boye Asirin Gwamnati da za su hukunta duk wani jami'in gwamnati wanda ba tare da an ba shi izini ba, ya ba wani mutum wani bayani da yake da yakini ya yi haka ne don ya nuna-

(a) keta wata doka ko ka'ida

(b) almubazzaranci ko tafka barnar kudi, ko almundahana da amfani da mukami ba daidai ba; ko

(c) gagaruma ko wani babban hadari da zai shafi lafiyar jama'a ko tsaron rayukansu, ko da wannan bayani ba a bayar da shi bisa tanadin wannan doka ba.

(3) Ba za a tuhumi wanda ya karbi bayanin da ya shafi aikata karami ko babban laifi ba, haka wanda ya dada watsa bayanin.

28. (1) Duk wani bayani da ke karkashin kulawar wata hukuma ta gwamnati, wannan hukuma tana ajiye da shi ne a karkashin kayayyakin da ake ba su tsaro na musamman ko tabbatar da tsaronsu a karakashin Dokar Boye Asirin Gwamnati, sai dai hakan bai tsame su daga neman a bayar da bayaninsu ba, idan aka rubuta bukatar neman bayanin a karkashin wannan doka, sai dai a kowane hali hukumar gwamnati da aka rubuta mata bukatar za ta yanke shawara ko wancan bayani yana cikin irin wadanda sassa na 11 da 12 da 14 15 da 16 da 17 da 19 da 20 da kuma 21 suke nufi.

(2) Idan hukumar gwamnatin da aka rubuta mata takardar bukatar da ke karamin sashi na (1) ta yanke shawarar cewa wancan bayani ba irin wanda aka ambata a karamin sashi na (1) ba ne, wajibi ne a ba mai nema damar samun wannan bayani.

(3) Idan hukumar gwamnati da aka mika mata takardar bukatar da aka ambata a karamin sashi na (1) ta yanke shawarar cewa wancan bayani yana cikin wadanda aka ambata a karamin sashi na (1), sai ta bayar da sanarwa ga mai neman bayanin.

29. (1) Wajibi ne kowace hukumar gwamnati ta mika rahoto ga Antoni Janar na Tarayya a ranar ko kafin ranar 1 ga Fabrairu na

kowace shekara, kan abin da ya kunshi harkokin kudinta na shekara wanda kuma zai hada da-

(a) yawan yunkurin da hukumar ta yi na kin bin amincewa da takardar neman bayani da aka mika wa hukumar da kuma dalilan daukar wadannan matakai;

(b) yawan daukaka kara da mutane suka yi a karkashin wannan doka da dalilin kin bayar da bayanin da ya jawo daukaka karar;

(c) bayyana ko kotun ta amince da shawarar hukumar na boye bayanin a wannan hali da kuma bayani dalla-dalla kan irin bayanin da aka ki bayarwa;

(d) yawan takardun neman bayanan da ke hannun hukumar har zuwa ranar 31 ga watan Oktoba na shekarar da ta gabata da matsakaitan yawan kwanakin da wadannan bukatu suka yi a hannun hukumar zuwa wannan rana;

(e) yawa ko takardun bukatun neman bayani da hukumar ta karba da kuma yawan takardun bukatun da ta yi aiki a kansu;

(f) matsakaitan ranakun da ta hukumar ta dauka wajen aiki a kan mabambantan takardun da ake bukatar bayanansu;

(g) yawan kudin da hukumar ta karba domin yin aiki a kan wadannan bukatun neman bayani; da

(h) yawan cikakkun ma'aikatan hukumar gwamnatin da aka ba aiki kan takardun bukatun neman bayani da kuma yawan kudin da hukumar ta kashe kan aiki a kan wadannan bukatun neman bayanin.

(2) Wajibi ne kowace hukumar gwamnati ta samar da wannan rahoto a wadace ga jama'a ta wadansu hanyoyi da suka hada

da na'urar kwamfuta da tarho, idan kuma gwamnati ko hukumar ba su da kwamfuta ko tarho, to, su samar ta waxansu hanyoyin sadarwa masu aiki da wutar lantarki.

(3) Antoni Janar zai samar da kowane rahoto da aka mika masa a wadace ga jama'a a bugaggun takardu da intanet da kuma ta hanyar sadarwa mai aiki da lantarki.

(4) Antoni Janar zai sanar da shugaba da wakilin marasa rinjaye na Kwamitin Sanya Ido kan Sauye-Sauyen Harkokin Gwamnati na Majalisar Tarayya da shugaba da wakilin marasa rinjaye na Kwamitin Harkokin Gwamnati da na Shari'a na Majalisar Dattawa akalla zuwa watan Afrilun shekarar, wanda a cikin rahoto da za a mika za a bayyana samuwar rahoton a kuma samar musu shi wadace a bugaggun takardu da kuma hanyar sadarwa mai aiki da lantarki.

(5) Antoni Janar zai bunkasa jagoran yadda ake bayar da rahoto da auna aiki dangane da rahotannin da wannan sashi ya nema kuma yana iya kara wadansu abubuwan da ake bukata kan wadannan rahotanni kamar yadda Antoni Janar din zai yanke shawara kan amfaninsu.

(6) Domin sauke nauyin da ke kansa a karkashin wannan doka, Antoni Janar zai tabbatar duk hukumomin gwamnati da wannan doka ta shafa sun yi aiki da tanade-tanaden dokar.

(7) Antoni Janar zai mika wa Majalisar Dokoki ta Kasa rahoton shekara-shekara a ranar ko kafin ranar 1 ga Afrilun kowace shekara wanda zai kunshi na shekarar baya da jerin yawan shari'o'in da suka taso a karkashin wannan doka da wadanda aka tsame daga cikin shari'o'i da shari'o'in da aka kammala da kudin da aka kashe da kudin da aka samu da kuma tarar da aka ci.

(8) Wannan rahoto har wa yau zai kunshi dalla-dallar yunkurin da Ma'aikatar Shari'a ta yi na karfafa wa dukkan hukumomin gwamnati kan su yi aiki da wannan doka.

(9) Ma'anonin kalmomi masu zuwa a karkashin wannan sashi-

(a) "gwamnati" ta hada da duk wani sashi mai ikon zartarwa da sashin sojoji da kamfanin gwamnati da kamfanin da gwamnati ke da jari a ciki da sauran hukumomi da ma'aikatun da suke bangaren zartarwa na gwamnati (ciki har da Ofishin Shugaban Qasa) da duk sauran bangarorin gwamnati masu zaman kansu da hukumar tsara doka ko duk wata cibiya ta gwamnati; da

(b) "bayani" na nufin duk wata ma'ana da aka yi amfani da ita a wannan doka da ke nuni ga bayani ko adanannen bayani da ya kunshi duk wani bayani da gwamnati ko wata hukumar gwamnati za ta iya rikewa da bayanin da ya gangaro a karkashin wannan doka lokacin da wata hukumar gwamnati take kula da shi a kowane irin fasali ciki har da wanda ke cikin na'ura mai aiki da lantarki.

(30) (1) Wannan doka manufarta ta karfafa ba ta maye hanyoyin ba jama'a damar samun bayanan da suka shafi takardu ko bayanan da suka shafi gwamnati da aka adana ba ne, kuma ta kowace hanya ba ta nufin ta takaita irin bayanan ayyukan gwamnati da jama'a ke samunsu a kowane lokaci.

(2) Idan aka samu takaddama kan ko a samar da wadansu adanannun takardu ko bayani na gwamnati, idan batun da ake magana ya fado a karkashin wannan doka ce, za a yanke hukunci ne kan batun kamar yadda yake kunshe a tanade-tanaden wannan doka, sai idan an samu cewa wannan doka ce ta tsame batun.

31. A cikin wannan doka-

“mai nema” yana nufin duk mutumin da ya rubuta takardar bukatar neman bayani a karkashin wanan doka;

“takardar bukata” tana nufin duk wata takardar neman bayani da aka nema a karkashin wannan doka;

“kotu” na nufin Babbar Kotu ko Babbar Kotun Tarayya;

“wata kasa” na nufin duk wata kasa baya ga Jamhuriyyar Tarayyar Nijeriya;

“bayani” ya hada da takardu da bayanan da aka adana ta kowace irin hanya, ciki har da rubutattu da wadanda ke cikin na’ura mai aiki da lantarki da hotuna da murya da aka nada a kaset da makamantansu.

“hukumar gwamnati” na nufin duk wata cibiyar gudanarwa da ta shafi bangaren majalisa da na zartarwa da na shari’a ko wata hukuma ta bayar da shawara ta gwamnati, ciki har da hukumominn gudanarwa da kwamitoci da hukumomin ma’aikatu na qasa da duk wani reshe na wadannan hukumomi ciki har da kwamitoci da kananan kwamitoci da ake amfani da kudin gwamnati wajen daukar nauyinsu baki daya ko wani bangare na aikinsu, ko wadanda ake ba kudin gwamnati suna gudanar da ayyuka ga jama’a ko suna wakiltar gwamnati ko suna sarrafa kudaden gwamnati da sauransu.

“adanannun bayanai ko takardu” na nufin kowane adanannen bayanai a kowane irin tsari da aka shirya ko aka yi amfani da shi ko aka karba ko aka mallaka ko yake karkashin kulawar duk wata hukuma ta gwamnati ko cibiyar gwamnati mai zaman kanta da take da alaka da al’amuran da suka shafi bukatun jama’a kuma sun kunshi-

(a) rubutu a kan kowace takarda;

(b) bayanin da aka adana ko aka ajiye ko wata na'ura; da dukkan wani abu da aka samu daga bayanin da aka adana ko aka ajiye;

(c) takarda ko kwali da aka lika don sanarwa, ko wani rubutu da ya gano ko ya yi bayanin wani abu da ya zama wani bangare ko aka hada shi da wata ma'ana;

(d) littafi ko kati ko fom ko taswira ko tsarin gini ko zanen girafik ko zane mai hoto;

(e) hoto ko fim ko dodon hoto ko dodon fim ko tef ko wata dabara ko na'ura da a ciki za a samu hoto daya ko fiye da za a iya (tare ko ba tare da wani abin taimako ko na'ura ba) a sake buga su.

"Minista" yana nufin Ministan da aka dora wa alhakin bayar da bayanin;

"mutum ko wani" ya hada da hukuma ko rukunin mutane, ya-alla a wuri daya suke ko a wurare daban-daban, da suke aiki a daidaikunsu ko a kungiyance;

"sirrin rayuwar mutum" na nufin duk wani bayanin hukuma da aka samu kan wani mutum da aka sani, amma bai kunshi bayanin da ya shafi aikin gwamnati na ma'aikatar hukumar gwamnati ko jami'an gwamnatin ba.

32. Wannan doka za a kira ta da Dokar 'Yancin Samun Bayanai ta Shekarar 2011.

NA TABBATAR, KAMAR YADDA SASHI NA 2 (1) NA DOKAR TABBATAR DA SAHIHANCI MAI LAMBA CAP A2 TA DOKOKIN JAMHURIYAR NIJERIYA TA 2004 YA TANADA CEWA WANNAN SHI NE GANGARIYAR KWAFE NA KUDIRIN DOKAR DA ZAURUKAN MAJALISAR DOKOKI TA KASA SUKA AMINCE DA SHI.

SALISU ABUBAKAR MAIKASUWA, mni

AKAWUN MAJALISAR DOKOKI TA KASA

27 GA MAYU, 2011

I CERTIFY, IN ACCORDANCE WITH SECTION 2 (1) OF THE ACTS AUTHENTICATION ACT, CAP. A2, LAWS OF THE FEDERATION OF NIGERIA 2004, THAT THIS IS A TRUE COPY OF THE BILL PASSED BY BOTH HOUSES OF THE NATIONAL ASSEMBLY.

SALISU ABUBAKAR MAIKASUWA, mni
CLERK TO THE NATIONAL ASSEMBLY

27th DAY OF MAY, 2011.

**Rataye kan Kudirin Dokar ʼYancin Samun Bayanai ta 2011**

| SUNAN KUDIRIN A TAKAICE | DOGON BAYANI KAN KUDIRIN | TAKAITACCEN BAYANI KAN ABIN DA KUDIRIN YA KUNSA | RANAR DA MAJALISAR DATTAWA TA AMINCE DA ITA | RANAR DA MAJALISAR WAKILAI TA AMINCE DA ITA |
|---|---|---|---|---|
| **DOKAR ʼYANCIN SAMUN BAYANAI TA 2011** | Doka ce da za ta sa adanannun takardu da bayanai su zamo a wadace kuma a ba jama'a damar iya samunsu babu matsala, kuma ta kare adanannun takardu da bayanan ayyukan gwamnati ta yadda za su dace da bukatun al'umma da kare sirrin rayuwar daidaikun mutane, kuma ta kare ma'aikaci daga musgunawar da za ta auku gare shi saboda bayar da bayanan da suka shafi hukuma ba tare da izini ba, kuma ta tsara hanyoyin da za a bi don cimma wadannan manufofi da abubuwan da suka danganci haka. | Wannan Kudirin Doka na so ya sa adanannun takardu da bayanai su dada zamowa a wadace kuma a ba jama'a damar iya samunsu babu matsala, kuma ya kare adanannun takardu da bayanai ta yadda za su dace da bukatun al'umma da kare sirrin daidaikun mutane da kare ma'aikaci daga musgunawa saboda bayar da wadansu bayanai da suka shafi hukuma ba tare da izini ba, kuma ta tsara hanyoyin da za a bi don cimma wadannan manufofi. | 24 ga Mayu, 2011 | 24 ga Mayu, 2011 |

Na tabbata ni da kaina na bi wannan Qudirin Doka a tsanake tare da matsayar da Majalisar Dokoki ta Qasa ta cimma, kuma na gano ita ce gangariyar matsaya sahihiya da Majalisar ta cimma, kuma hakan ya dace da abin da ke kunshe a cikin Dokar Tabbatar da Sahihanci, mai lamba CAP A2 ta Dokokin Tarayyar Nijeriya na shekarar 2004.

**SALISU ABUBAKAR MAIKASUWA, mni**

Akawun Majalisar Dokoki ta Kasa

27 ga Mayu, 2011

Na sanya hannu a kai.

**DOKTA GOODLUCK EBELE JONATHAN,** GCFR

Shugaban Jamhuriyyar Tarayyar Nijeriya

28 ga Mayu, 2011.

**Schedule to Freedom of Information Bill, 2011**

| SHORT TITLE OF THE BILL | LONG TITLE OF THE BILL | SUMMARY OF THE CONTENTS OF THE BILL | DATE PASSED BY THE SENATE | DATE PASSED BY THE HOUSE OF REPRESENTATIVE |
|---|---|---|---|---|
| **Freedom of Information Bill, 2011** | An Act to make public records and information more freely available, provide for public access to public records and information, protect public records and information to the extent consistent with the public interest and the protection of personal privacy, protect serving public officers from adverse consequences for disclosing certain kinds of official information without authorization and establish procedures for the achievement of those purposes and; for related matters. | This Bill seeks to make public records and information more freely available, provide for public access to public records and information, protect public records information to the extent consistent with the public interest and the protection of personal privacy, protect serving public officers from adverse consequences for disclosing certain kinds of official information without authorization and establish procedures for the achievement of those purposes. | 24th May, 2011 | 24th May, 2011 |

I certify that this Bill has been carefully compared by me with the decision reached by the National Assembly and found by me to be true and correct decision of the Houses and is in accordance with provisions of the Acts Authentication Act Cap, A2, Laws of the Federation of Nigeria, 2004.

I ASSENT.

**SALISU ABUBAKAR MAIKASUWA, mni**
**Clerk to the National Assembly**
**27th Day of May, 2011**

**DR. GOODLUCK EBELE JONATHAN, GCFR**
**President of the Federal Republic of Nigeria**
**28th Day of May, 2011**

**Wallafar**

R2K RIGHT TO KNOW ...YOUR LIFE DEPENDS ON IT

Da taimakon

OPEN SOCIETY INITIATIVE FOR WEST AFRICA